Hukumar Soja ta Amurka ga sashen Afrika
Ofishin Harkokin Jama'a

**Tarihin mutum**

## Janar William E. "Kip" Ward

*Hukumar Soja ta Amurka ga sashen Afrika*

---



Janar William E. (Kip) Ward ya zama kwamanda na farko na Hukumar Soja ta US ga sashen Afrika a Stuttgart, kasar Jamus, a farkon watan Oktoba, 2007. Hukumar Soja ta US ga sashen Afrika ita ce daya cikin hadadden hukumomin soja a sassan duniya a cikin tsarin hadadden hukumomi soja na Hukumar Tsaron Kasa.

Janar Ward ya fara aikin soja cikin Dakarai a Yuni 1971. Karatun soja gare shi ya hada da kwas na Kasa da na Sama ga Hafsan Dakarai, Jami'ar Hukumar Rundunar Soja ta US da Ma'aikatan Soja, da kuma Jami'ar Yaki na Rundunar Soja ta US. Ya rike Digiri na Biya a fannin Ilimin Siyasa daga Jami'ar Pennsylvania State da kuma Digiri na Farko a fannin Ilimin Siyasa daga Jami'ar Morgan State. Aikinsa na soja ya hada da rangadi a kasashen ketare a Koriya, Masar, Somaliya, Bosniya, Israyel, rangadi biyu a Jamus, da kuma ayyuka iri-iri a Amurka, har da Alaska da Hawaii.

Ayyukansa hukumar soja da runduna sun hada da: Shugaban Bangaren Soja, Bataliya ta 3 (Mayakan Sama), Dakarai na 325, Bangaren Mayakan Sama na 82, a Fort Bragg, North Carolina; Kwamandan Kamfanin Masu Bindiga, Bataliya ta 1 (Na Inji), Dakarai na 17, Bangaren Dakarai na 2, a Camp Howze, Korea; S-4 (Dabaru), Birgedin Igwa a Fili na 210, VII Corps, Rundunar Soja ta US a Turai da Rundunar ta Bakwai, a kasar Jamus; Babban Hafsa, Bataliya ta 1 (Na Inji), Dakarai na 7, Bangaren Dakarai na 3, Rundunar Soja ta US a Turai da Rundunar ta Bakwai, a kasar Jamus; Kwamanda, Bataliya ta 5, Dakarai na 9, Birgedi na 2, bayan haka G-4 (Dabaru), Bangaren Dakarai na 6 (Karamar Igwa), a Fort Wainwright, Alaska; Kwamanda, Birgedi na 2, Bangagen Dutse na 10 (Karamin Igwa), a Fort Drum, New York da kuma Shirin Mayar Sa Rai, a Mogadishu, kasar Somaliya; Mataimakin Kwamandan Bangare (Goyon Baya), Bangaren Mayakan Sama na 82, a Fort Bragg, North Carolina; Kwamandan Janar na Bangaren Dakarai na 25 (Karamar Igwa) da na Rundunar Soja ta US, Hawaii, a Schofield Barracks, Hawaii; da kuma Kwamanda, Rundunar Zaman Lafiya, Shirin

Hadadden Makera, a Sarajevo, Bosniya.

Ayyukansa na ma'aikata sun hada da: Babban Hafsa, Aikace-aikacen Jama'ar Soja na Rundunar Soja ta US -- Aschaffenburg, Rundunar Soja ta US a Turai da Rundunar ta Bakwai, a kasar Jamus; Hafsan Ma'aikata (Dabaru), Ofishin Mataimakin Hafsan Hafsoshi ga Shirye-shirye, Rundunar Soja ta US, a Washington, DC; Babban Hafsa wa Mataimakin Hafsan Hafsoshi, Rundunar Soja ta US, a Washington, DC; Mataimakin Darakta ga Shirye-shirye, J-3, Cibiyar Hukumar Soja na Kasa, Hukumar Joint Staff, a Washington, DC; Shugaba, Ofishin Hadin Gwiwan Soja, Masar, a ofishin jakadanci na Amurka, a Masar; da kuma Mataimakin Darakta ga Shirye-shirye, J-3, Hukumar Joint Staff, a Washington, DC.

Gabannin shigowar mukaminsa na yanzu, Ward ya rike mukamin Mataimakin Kwamanda, Hedkwatan Hukumar Soja ta US ga sashen Turai, a Stuttgart, Jamus. Da ya yi aika a mukamin Mataimakin Kwamandan Janar/Hafsa Hafsoshi, Rundunar Soja ta US a Turai da Rundunar ta Bakwai. A lokacin da ya rike mukamin nan Sakatare na Harkokin Waje ya zabe shi don ya zama Mai Kula da Tsaro na Amurka ga Israyel - Hukumar Falasdinawa inda ya yi aiki daga Maris zuwa Disamba 2005.

Lambobi da bajoji da Janar Ward ya samu sun hada da: Lambar Mashahurin Aiki Tsaro (da Damin Ganyayen Oak); Lambar Mashahurin Aiki; Lambar Mafificin Aikin Tsaro (da Damai Biyu na Ganyayen Oak); Rundunar Amfani (da Damai Uku na Ganyayen Oak); Lambar Aiki mai Amfani na Tsaro; Lambar Aiki mai Amfani (da Damai Shida na Ganyayen Oak); Lambar Yabon Hadin Aiki; Lambar Yabo na Rundunar Soja (da Damai Uku na Ganyayen Oak); Lambar Cimma Buri ta Rundunar Soja (da Damin Ganyayen Oak); Bajon Gwanin Dan Dakarai; Bajon Dan Dakarai na Daga; da kuma Bajon Gwanin Dan Yin Saukar Laima.